# Ka Kusaci Allah Cikin Addu'a (Sashe na 1)

An ɗauko daga babi na 17 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?* za a iya samunsa a dandalin jw.org/ha.

**MANUFA: Ka bincika abin da ka yi imani da shi da kuma dalilin da ya sa ka yi hakan, kuma ka bincika abin da Littafi Mai Tsarki ya koyar don ka iya bayyana wa wasu abin da ka yi imani da shi.**



## SHIN, ALLAH YANA JIN KOWACE IRIN ADDU'A NE?

### 1 KA BINCIKA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

Me ya sa wasu mutane za su ce e?

Me ya sa wasu mutane za su ce a'a?

Me *ka* yi imani da shi?

Me ya sa ka yi imani da hakan?



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 2 KA BINCIKA ABIN DA LITTAFI MAI TSARKI YAKE KOYARWA

**Allah yana jin addu'ar waɗanda suke masa biyayya, ko da mene ne suka roƙe shi.**

(Ka duba babi na 17, sakin layi na 1-4 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

### Karanta Filibiyawa 4:6, 7.

Kari ga yin addu'a a lokacin da muke bukatar wani abu, me ya sa ya dace mu gode wa Jehobah sa'ad da muke addu'a a kowane lokaci?

___

___

___

### Karanta Yaƙub 4:8.

Ta yaya yin addu'a yake ƙarfafa dangantakarmu da Jehobah?

___

___

___



**Dukanmu muna son abokan da suke mana magana a kowane lokaci ba sai lokacin da suke bukatar wani abu ba. Haka yake da Jehobah, yana so mu riƙa yin magana da shi a kowane lokaci, kuma a kan batutuwa dabam-dabam**



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## Allah yana jin addu'ar waɗanda suke ƙoƙartawa su yi rayuwar da ta jitu da abin da suka yi addu'a a kai.

(Ka duba babi na 17, sakin layi na 5-8 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

### Karanta Markus 11:24 da Yaƙub 2:26.

Me ya sa muke bukatar mu kasance da bangaskiya kafin Allah ya ji addu'armu, kuma ta yaya za mu nuna cewa muna da bangaskiya?

### Karanta Matta 6:11 da 2 Tasalunikawa 3:10.

Ka ba da misalin yadda za mu iya yin abin da ya jitu da addu'armu.

Shin, *kana* godiya domin Allah ya ba ka gatan yin addu'a? Me ya sa?


www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 3 KA BAYYANA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

IDAN WANI YA CE. . .

**Allah yana jin kowane irin addu'a.**

ZA KA IYA CE. . .

**Mutane da yawa sun yi imani da hakan. Amma Littafi Mai Tsarki bai koyar da hakan ba domin. . .**

______________________________

______________________________

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

______________________________

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

______________________________

IDAN WANI YA CE. . .

**Addu'a abu ne da mutum yake yi idan yana son zuciyarsa ta kwanta.**

ZA KA IYA CE. . .

**Wataƙila mutane da yawa za su yarda da hakan, amma ban yarda da hakan ba domin. . .**

______________________________

______________________________

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

______________________________

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

______________________________



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania